# Hausa wikipedia

## Hausa Wikipedia Insakolopiya ce ta kyauta

## Mukaddiman Hausa Wikipedia

Insakolopidiya ce wacce kowa zai iya gyarawa

Hausa Wikipedia ta kasance insakolopidiyace ta kyauta wacce kowa da kowa zai iya yin rejista domin taimaka ma yaran harshen Hausa da kuma Hausa Wikipedia, Wikipedia ce wacce take dauke da kundin ilimi na kowanne bangare, kuma ilimin mutane Kaman ku ne suke sakawa, saboda ilimi ya yadu a duniya baki daya amman a cikin harshen Hausa, kyauta ake amfani da duk ilimin dake Wikipedia, kuma kyauta ake saka ilimin domin taimaka ma yaran Hausa da Hausa Wikipedia, ita Hausa Wikipedia ana Kirkiran shafuka ne wato (Articles) da yaran Hausa, Kamar yanda kowanne yare suke da ta su Wikipedian, akwai English Wikipedia (en.english.org), Arabic Wikipedia (ar.english.org), Yoroba Wikipedia, (yo.english.org) Igbo (ig.english.org) Wikipedia dadai sauran su, kowanne Wikipedia a cikin wadannan yana rubuta Wikin sa ne da harshen yaran sa, shiyasa ma internet URL din ya ban banta da juna, akwai Wikipedia a yaruka sama da 300 a cikin Wikipedia, kowanne a ciki ana kiran shi da **Wikipedia.** A dalilin haka ne yasa Hausa Wikipedia ke bukatar al'uman Hausawa da suyi rejista domin taimaka ma yaran Hausa da kuma Hausa Wikipedia, yin rejista ko shiga shafin Wikipedia a yanar gizo kyauta ne, kawai ka rubuta ha.wikipedia.org a burauzan ka domin shiga babban shafin hausa Wikipedia, kana shiga zaka ga inda zaka iya yin rejista

**YIN REJISTA A HAUSA WIKIPEDIA KYAUTA NE, DOMIN SAKA ILIMI KYAUTA, KO AMFANI DA ILIMIN KYAUTA.**

### A takaice

Hausa Wikipedia **insakolopidiya** ce ta kyauta wanda hukumar Wikimedia Foundation suke dauka nauyi, domin yada ilimi kyauta ga duniya a cikin harsunan duniya harma da yaran Hausa, shiga Hausa Wikipedia ko yin rejista **kyauta** ne a ha.wikipedia.org, sannan Kirkiran shafi ko gudunar da sauye-sauye ma kyauta ne, domin yada ilimi kyauta ga duniya, musamman ma a cikin harshen Hausa, zaka/zaki iya yin rejista domin yaran Hausa da Hausa Wikipedia ta cigaba,

# Kirkiran Akount

## Yanda ake Kirkiran akount

Kirkiran akount a Hausa Wikipedia kyauta ne, kuma shiga cikin Wikipedia domin Kirkiran akount shima kyauta ne, ka/ki rubuta ***ha.wikipedia.org*** a cikin burausan ka/ki domin shi babban shafin Hausa Wikipedia, da zaran ka shiga ciki, zaka ga a sama an saka maka **ku kirkiri akount,** sai ka danna wannan link din domin shiga inda zaka kirkira akount, yana budewa sai ka zaba suna(Username) da kalmomin sirri wato (Passwoord), sannan ka sanya rubutun tantence cewa kai ba sakago bane, wato (Robot), da zaran kayi hakan sai ka danna abunda ke kasa domin Kirkiran akount a Hausa Wikipedia, idan kuma kana san bidiyo akan yanda ake Kirkiran akount kama wannan numban Magana a Whattsapp domin turo maka bidiyoyin koyan Hausa Wikipedia ta Whattsapp.

**<u>Wasu daga cikin hotunan da zasu nuna muku hanyan da zaku bi domin yin rejista.</u>**

Ku rubuta ha.wikipedia.org a burauzan ku, zai nuno muku wannan shafin, wanda shine babban shafin Hausa Wikipedia, sai ku dannan inda wannan aran manuniyan ya nuna.




Ku danna wannan_link din domin shiga inda zaku kirkira akount, in kuka danna, wannan shafin dake kasa zai fito.




## Bude akount

- ❶ Ku zaba suna wato (Username).
- ❶ Ku zaba kalmomin sirri wato (Password) misali **Garbaty86**
- ❶ Ku saka adreshin i-mail dinku, misali **Gargabaty4563@gmail.com**
- ❶ Ku rubuta wadannan kalmomin domin tantan ce ku ba robot bane.
- ✓ Sai ku danna wannan domin kirkiran akount a Hausa Wikipedia

**A wannan shafin ne zaku cike abubuwa kaman haka:-**

- ❶ Ku zaba suna wato (Username) misali **Garbaaty**
- ❶ Ku zaba kalmomin sirri wato (Password) misali **Garbaty86**

- Ku saka adreshin i-mail dinku, misali **Gargabaty4563@gmail.com**


*DAGA ZARAN KA GAMA WANNAN TO KA ZAMA CIKAKKEN EDITA MAI REJISTA A HAUSA WIKIPEDIA.*
*ZAI NUNA MAKA SHAFI KAMAR HAKA.*




Barka da zuwa Hausa Wikipedia, insakolfidiy ce wacce kowa zai iya gyarawa, daga nan ne zaka fara gudunar da aikace aikace a matsayinka na edita mai rejista, amman kafin nan, bari in nuna mai karatu wasu daga cikin muhimman gurare a babban shafin Hausa Wikipedia.

# Abubuwa masu muhimmanci

Da farko da ana san edita ya san cewar kowanne abu da yake gani a gaban shafin Hausa Wikipedia na da amfanin sa, musamman ma a can sama da kasa, da kuma gefan dama.



## ➢ Daga Sama




1. **Username:** sunan amfani domin iya banbance ka da sauran editoci a Hausa Wikipedia, misalign sunan amfanin dake sama shine **Anasskoko**, duk wani edita a Wikipedia da wannan sunan zai sanka da shi. A nan ne User zai rubuta sunan shi da kuma wanene shi domin sauran editoci su samu saukin fahimtar sa. Idan baka rubuta komai ba a gurin, to zaka gan shi ya nuna launin ja ne, kamar haka Anasskoko idan kuma na rubuta bayanai a kaina zai nuna min launi kamar haka Anasskoko.
2. **Alaman kararrawa:** alaman kararrawa alama ce da idan aka turo maka da sakon sanarwa ta gaggawa zatayi sauri ta nuna maka tahanyar komawa JA, da zaran kaga haka to kana da sakon gaggawa. Sai kayi sauri ka danna kararrawan domin ganin sakon ka.
3. **Alaman allo:** alama ce dake nuna karamin sako a Wikipedia, ko kuma wani sako daga wana guri a Wikipedia, shi wannan alaman sakon bai kai alaman kararrawa muhimmanci ba, amman dai dukkan su sako dake sanar da kai wani abu.
4. **Talk:** wannan daya ne daga cikin muhimman gurare a Wikipedia, a cikin wannan talk dinne dukkannin editoci a Wikipedia, zas ringa yam aka Magana. Suna maka Magana za'a sanar da kai ta **Alaman kararrawa.** Idan kayi rubuta sako ko aka rubuto maka sako to anaso kayi signing a karshe, ta hanyan amfani da Tilde guda hudu, sune kamar haka ~~~~, idan kagama rubuta sako to ka tabbata ka rubuta wannan ~~~~, otomatikally zai canza ya maida shi sunanka da (Username) shafinka na Magana (Talk), kwanan wata (Date), da kuma lokaci (Time).

**A SANI:** indai baka rubuta haka ba ~~~~ bayan ka tura ma wani edita da sako to ba zai ga sunanka ba, a sani a na rubuta wannan ne kadai ~~~~ idan za'a tura sakon Magana, ko amasa Magana, koyi zabe, da duk abinda yafi tattaunawa a Wikipedia.

**A SANI:** ba'a rubuta wannan a gun rubuta mukala wato (Article).

5. **Beta da Preference:** a nan ne edita zai sanya wasu Karin kayan aiki a Wikipedia domin gudanar da aikace aikace, a sani wannan abubuwan suna da matukar hatsari ga dan koyo.

6. **Watchlist:** Dukkannin shafukan da kayi makin din su domin karinga gadin su ta nanne zaka gansu.
7. **Contrubutions:** a nanne edita zai ringa ganin dukkannin aikin da yake yi a Hausa Wikipedia, tin daga ranar da yayi rejista. Sannan ta nan ne edita zai iya fassara mukala daga wani yare zuwa wani yare, ta hanyar danna **Translations**, har wayau ta nanne edita zai iya saka fayel a Hausa Wikipedia ta hanyar danna **Uploaded Media**.

## ➢ Daga Kasa




Daga kasa akwai wasu muhimman bayanai dake nuna amfanin gudanarwa a Hausa Wikipedia, sune kamar haka:

1. **Privacy Policy:**
2. **About Wikipedia**
3. **Disclaimers**
4. **Mobile view**
5. **Developers**
6. **Statistics**
7. **Cookie statement**


Dukkanni wadann nan suna muhimmanci edita ya shiga ya duba su domin fahimtar Wikipedia sosai da sosai, amman akwai wanda zanyi bayanin sa mai muhimmanci ga editoci, shine “**Mobile view**”

- **Mobile view:** Yana da matukar muhimmncin gaske mutum yasan menene **Mobile view** da kuma **Destop,** duba shafin kasa domin samun cikakken bayani akan hakan.

**Mobile view** da kuma **Desktop**, salo ne na yanda shafi ko faji zai ringa nuna maka a wayan ka ko kuma komfutan ka, asali Mobile view na wayar hannu ne, desktop kuma nakura mai kwa kwalwa ne wato komfuta.amman yanzu a wikipedia  zaka iya saka duk wadanda kake so.

***Mobile view na wayar hannu ne, destop kuma na komfuta, amman zaka iya saka duk wanda kake so a nakuran da kake amfani da shi.***

**Yanda yake nunawa a nakuran da'ake amfani da shi.**





Wannan alama ce dake nuna cewar intafes dinka yana kan **Desktop,** shiyasa ya nuna maka **Mobile view** kamar da yanda wancan aran yake nuna maka, ma'ana idan ka danna zai koma **Mobile view** kenan.

- **Desktop:** ne mafi saukin amfani, kuma mafi nagarta, saboda zai nuna maka komai a zahiri kuma a fili batare da ka sha wahala ba wajan gano abubuwa, yana nuna edita komai a fili ba tare da edita ya sha wahalan nemo w aba, sannan shafuka suna nuna hotuna, video da sauti a fili, sannan kyan destop yafi na mobile view, har way au dais hi desktop ya bama edita daman yayi amfani da wikipedia cikin sauki, kuma zaka iya saka destop a wayar hannu ko kuma komfuta, duk yana yi a kowanne, sai dai kawai idan a waya ne kana da bukatan ka ringa zoomin ciki da waje, kasancewar girman sikirin din waya bai kai na komfuta ba.


Idan ka shiga desktop zaka ga URL dinka ya nuna maka haka, “ha.wikipedia.org/wiki/user:Anasskoko” amman idan a mobile view yak e zai nuna maka haka “ha.m.wikipedia.org/wiki/user:Anasskoko” banbancin shine **“m”,** M din ma'anar sa shine Mobile view,

idan kana amfani da Desktop zai nun maka shafi kamar haka,




Kaga a wannan shafin kana ganin komai da komai da komai a fili, sannan kuma URL din a fili yake, zai nuna maka “ha.wikipedia.org/wiki/user:Anasskoko” , kuma shafukan amfani suna fili a farfajiyan babban shafin Hausa Wikipedia, munyi bayanin abubuwa daya daga cikin wadannan shafin.

- **Mobile view:** shine wanda ake amfani da shi a wayar hannu, anyi mai tsare tsare n domin ya kasance daidai da wayar hannu, dan editoci masu amfani da wayar hannu, amman hakan bai hana bama edita daman komawa **Desktop** ba, idan kana so ka koma Destop sai ka danna wannan alama da aran nan ya kalla.




Ka danna wanna link din domin komawa **Desktop,** sannan ka kara danna Mobile view a nan domin komawa, kamar haka.




Idan ka danna wannan link din zai maid aka **Desktop,** kada ka rude da sunan da ka gani a rubuce, domin yana nuna sunan da zaka koma ne, ba sunan da kake kai ba, amman yawancin kwararrun editoci sunfi amfani da Desktop, domin kwarewa wajen editin da kuma gudanar da aikace aikace cikin sauki, da kuma sauri, batare da jinkira ba, sannna akwai abubuwan da a fili suke koda yaushe idan Desktop ne, amman a Mobile view wasu abubuwa a boye suke saika nemo su.

| SHAWARA |
| --- |
| DA SO SAMU NE EDITA YA SABA MA KANSHI DA AMFANI DA DESKTOP, DOMIN SHINE MAKURA A AMFANI |

Da fatan zaku yi rejista a ha.wikipedia.org

## Daukan nauyi

Wannan furojet din ya samu tallafi ne daga **Wikimedia Foundation** da kuma **Hausa Wikimedian User Group**

English

## Sponsored by

This project is sponsored by **Wikimedia Foundation** and **Hausa Wikimedian User Group**